# Yi Gwaji da Rigakafin Hepatitis B (Hep B)!

## Kare kanka da masoyanka

Domin neman wajen gwaji ko rigakafi, kira **311** yi tambayan "Hepatitis B" ko a ziyarci **nyc.gov/health/hepb.**

Hausa 10.20

# Yi rigakafin Hep B!

Hep B cuta ce me shiga hanta kuma ta haifar da ciwon hanta, cutar daji ko mutuwa. Akan yada da cutar Hep B daga mutum daya zuwa wani ta hanyar jini, maniyi ko ruwan cikin al'aurar mace.

Cutar ba ta da magani, amma rigakafin na da aminci kuma zaya iya kareka daga kamuwa da Hep B. Sai ka cika tsarin sha na biyu-biyu ko uku-uku kafin ka sami cikakken kariya.

Cike ranakun rigakafin Hep B dinka.

| | | |
|---|---|---|
| Ranar karban rigakafi 1 | / / | |
| Ranar karban rigakafi 2 | / / | |
| Ranar karban rigakafi 3 | / / | |

# Yi gwaji don sanin matsayin cutar Hep B a jikin ka!

Mutum 230,000 a Birnin New York suna rayuwa da cutar Hep B amma ba lallai bane su sani kuma ba za su ji shi ko nuna alaman ciwo.

Mafi yawa masu wanan cutar Hep B sun kamu a lokacin haihuwa. Wadansu hanyoyin yau-da-kullum na kamuwa da wannan cutar sune rabawa ko sake amfani da allurai, sirinji ko kayan aikin asibiti, ko jima'i ba tare da kariya ba.

Ganowa da wuri da kuma samun kula wajen mai kulawa da cutar Hep B suna da muhimmanci wajen taya ka samun rayuwa mai tsawo da cikakken lafiya.